# BAYANI AKAN ZAMA WAKILI NA MUSAMMAN KO QWARARRE A BISA TSARIN DOKA

## Me ake nufi da wakili bisa tsarin doka?

Sha'anin gwajin magani, yakan janyo yin amfani da wani tsari na doka domin kare haqqin mutanen da ba za su iya yanke shawara a qashin kansu ba. Wannan batu ya haxa da samawa kai kariya lokacin gudanar da bincike akan mutanen da a wani sa'i ko kuma a kullum ba za su iya bayyana amincewarsu ba saboda matsalar rashin lafiya: misali matsananciyar jinya ko suma ko rashin ilmi ko buguwar kai ko kuma tavin hankali. Ta wannan fuska, tsarin dokoki na gwajin magani yana buqatar cewa kafin a sanya mutumin da ba zai iya bayyana amincewarsa ba a cikin tsarin gwajin, tilas a samo wani mutum da ya dace wanda zai amince a matsayin wakili bisa tsarin doka kafin saka shi wancen mutum cikin gwaji. Ana baka/ki wannan bayani ne saboda qungiyar masu bincike ta zabe ka/ki a matsayin wakili bisa tsarin doka. Wannan takarda da sauran takardu da ke biye, waxannda suke qunshe da bayanin masu sha'awar shiga wannan shiri, za su bayyana maka abin da wannan bincike ya qunsa kai da majinyacin

## Me ya sa aka tinkare ni?

Wakili bisa tsarin doka shi ne duk wani mutum da yake da alaqa kai-tsaye da shi majinyacin kuma ba su da savani a ra'ayi, kamar ya kasance yana cikin qungiyar masu bincike ko kuma mai neman kuxi. Irin mutanen da suka dace da wannan aiki su ne kamar haka;

- Xan cikin iyali ko mai xaukar nauyi ko kuma aboki.
- Mataimakin da kotu ta naxa wanda ke da alaqa da mai sha'awar shiga shirin.

Idan aka bi duk matakan da suka aka sani amma ba a samu wakili bisa tsarin doka ba, mai bicike sai ya naxa wani wanda zai tsaya a madadin majinyaci.Wannan mutum shi ne zai shiga sha'anin majinyaci, sai dai tilas ya zama ba shi da alaqa da aikin binciken. Shi kuwa mutumin da ya dace ya zama qwararren wakili bisa tsarin doka shi ne likita mai zanman kansa da yake yi wa majinyaci aiki ko kuma mutumin da hukumar lafiya ta naxa.

## Mene ne aikin wakili bisa tsarin doka?

Baban aikin wakili bisa tsarin doka shi ne; ya bayyana matsayinsa na amincewa game da shigar da majinyaci cikin aikin binciken. Ana bayyana matsayi bisa zavin kai ne idan kuma ka/kika qi cewa komai ma, to tilas za a mutunta ra'ayinka/ki

Domin taimakonka/ki wajen yanke shawara kan zama wakili bisa tsarin doka da kuma taimakawa wejen yake shawarar amincewa, akwai kevantacciyar takarda da ke bayyana wa mai sha'awar shiga shirin duk abin da wannan gwaji ya qunsa. Wannan bayani shi za a yi wa majinyacin da zan iya yanke shawara shi da kansa.

## Me zai faru idan na amince?

Idan har ka amince a madadin aboki ko xan uwa nan take ya shi wanda aka amince a madadinsa ya zama cikin waxanda za a dama da su a wannan gwaji. Takardar bayani wadda mai bincike zai maka qarin-haske, za ta nuna yadda abin yake dalla-dalla. Ko da kuwa ka amince yanzu, kana iya jenyewa a kowane lokaci nan gaba. Haka kuma idan aboki ko xan uwa da aka amince a madadinsa ya sami ikon Magana, yana da haqqi a tambaye shi ko zai cigaba da kasancewa a cikin wannan gwaji.